# Jagora Ga Iyaye Zuwa Ga Samun Gurbi, Bita, Da Matakan Kora

Janairu 2025



THE TEXAS LEGAL FRAMEWORK
for the Child-Centered Special Education Process
FW.ESCAPPS.NET

TEA Texas Education Agency
TEA.TEXAS.GOV/TEXASSPED

SPEDTEX Special Education Information Center
SPEDTEX.ORG

# Abubuwan da ke ciki

Gabatarwa ........ 2

JAGORA GA IYAYE ZUWA GA SAMUN GURBI, BITA, DA MATAKAN KORA ........ 3

Kula Da Kananan Yara a Matakin Farko ........ 3
Ayyuka ga Yara Yan Shekaru Uku Zuwa Biyar (kafin shiga ƙaramar makarantar boko) ........ 3
Taimako kan Shekarun koyon Yaro ........ 3
Shirin Tallafawa Mai Falle da Yawa, da ya shafi Amsa bukatar Neman Tallafi ........ 4
Turawa tantancewa matakin farko ........ 4
Gabanin Rubutacciyar Sanarwa ........ 5
Amincewar Iyaye ........ 5
Tsare-tsaren Tantancewa ........ 6
Tarukan Kwamitin Shiga, da Bita, da Kora (ARD) ........ 7
Cancanta ........ 8
Assasa Shirin Gatanci na Neman Ilmi (IEP) ........ 9
Na yanzu Matakin Nasarar Ilmi Ayukkan Himma ........ 10
Muradun Shekara ........ 10
Ilmi Na Musamman, Ayyuka Masu Alaka, da Karin Taimako da Ayyuka ........ 11
Bayyana Kimantawa ........ 11
Miƙawa ........ 11
Manyan Ɗalibai ........ 13
Yara Masu Galhanga ........ 13
Yara Kurame ko Masu Lalurar Ji ........ 13
Yara Makafi ko Masu Lalurar Gani ........ 13
Tsarin Gyaran Tarbiyya da Kulawa (BIP) ........ 14
Karin Lokacin Ayyukan Makaranta (ESY)14 ........ 14
Cike Gurbi ........ 14
Matakin Kwamitin ARD ........ 15
Kwafin IEP ........ 15
Sake Duban IEP ........ 16
Tantancewa ........ 16
Tantancewa Ilmi Mai Zaman Kanta (IEE) ........ 17
Janye Ayyukan Don Amicewa ........ 17
Kammalawa ........ 18
Ladabtarwa ........ 19
Saurаren Bahasi Na Gaggawa ........ 21
Sulhunta Jayayya ........ 21
Karin Taimako ........ 21

**Haƙkin Mallaka © 2025. Hukumar Ilmi ta Texas. Riƙon Duk Haƙkin Mallaka.**

## Gabatarwa

Hukumar Ilimi ta Texas (**TEA**) ce ta samar da wannan jagoran domin cika sharadin da ke cikin Kundin Ilmi na Texas §26.0081. An tsara wannan jagora don ya ba ka, a matsayinka na mahaifin yaro wanda ya ke ko zai iya cancanta samun ilmi na musamman da ayyuka masu dangantaka, kyakkyawar fahimtar lamarin ilmi na musamman sannan da tsarin haƙƙinka da ikonka saboda haka kana iya samun damar shiga cikin masu yanke hukunci dangane da ilmin yaronka.

Dokar Ilmi ta Masu fama da lalura ta musamman ta 2004 **(IDEA)** dokar tarraya ce da ke lura da sha'anin ilmi na musamman. Ɗaya daga manyan dalilai na IDEA shi ne tabbatar da cewa an samar ma yara masu fama da lalura ilmin al'umma a kyauta (**FAPE**) da ke ƙarfafa ilmi na musamman da ayyuka masu dangantaka da aka tsara don su dace da buƙatunsu sannan su shirya mu su tsarin ilmi, aiki, da dogaro da kai. *Ilmi na musamman* na nufin tsarn da aka yi don ya cimma wasu buƙatun yara masu fama da lalura. *Ayyuka masu alaƙa* na msamman ne da ake buƙata domin tallafawa ilmin ɗalibai na musamman don su ci gaba su cimma ƙudurorinsu na ilmi da aiki. Ayyuka masu alaƙa na iya haɗawa da aikin likita, aikin gyaran jiki, aikin nazarin magana da harshe, ayukan shawarwari, ayyukan horo da motsawa, da/ko ayyukan sufuri.

A bisa dokar IDEA, yana da muhimmanci ga iyaye su shiga a dama da su a dukkan matakan tsare-tsaren ilimi na musamman Wannan jagora kan bayyana ayyuka daban-daban da ka iya faruwa a lokacin sha'anin. Don ƙara taimaka ma fahimtar haƙƙoƙinka na shari'a a ƙarƙashin IDEA, akan nemi makaranta ta ba ka kwafin takardun da ake kira Sanarwar Tsare-tsaren Kariya (Kafa: fw.escapps.net) a wasu lokuta a cikin sha'anin ilmi na musamman. Dole ne a gabatar maku da takardar aƙalla sau ɗaya a shekara da kuma duk lokacin da ɗaya daga cikin waɗannan ya faru:

- Bayan maganar ko bukatarka don tantance farkon shigar yaronka;
- Bayan samun ƙorafin jiha na farko a cikin shekarar karatu;
- Bayan samun buƙatar farko na sauraron shari'a a cikin shekarar karatu;
- A ranar da aka yanke shawarar yin sauyin ladabtarwa na wuri; da
- Bisa ga buƙatarka.

Ana neman makarantar da ta ba ka takardar da ake kira *Bitar Ilmi na Musamman Domin Iyaye* da TEA ta samar, wadda akan ba ka idan tun farko an maida yaronka ƙarƙashin kulawar ilimi na musamman.

A Jihar Texas, alhakin yanke shawarar cewa yaro ya cancanci ilimi na musamman da kuma sauran ayyuka masu alaƙa da hakan, da kuma mafi yawancin zartar da shawara game da shirin ilimi na musamman na yara, to ya rataya ne a wuyan Kwamitin (**ARD**).shigar da ɗalibai da bitar halayensu da sallamarsu. Kana kuma iya sauraren wannan ƙungiya da aka bayyana da tawagar shirin ilmi na mutum **(IEP),** wanda shi ne sunan da ake amfani da shi a kotun tarayya. Idan aka samar da kwamitin ARD don yaronka, to za ka zama mamba na kwamitin.

Za a sabunta wannan jagora lokaci-lokaci a matsayin sauyi ga buƙatocin samarr da ilmi na musamman na tarayya da jaha ke faruwa. Samfurin na latironi da ake iya bugawa na samuwa a Yanki na 18 na shafin yanar gizo na Cibiyar Ilmi a Tsarin Shari'a na Ilmin Yara na Musamman (Kafa: fw.escapps.net).

Akwai kwanaki da dama da ranar ƙarshe ga tsarin ilmi na musamman. A cikin wannan wallafar, an bayyana waɗannan kwanakin da ranakun ƙarshen na musamman. Bugu da ƙari, akwai takarda abokiyar tafiya da za ta taimaka wajen amsa tambayoyi game da lokutan gwajin ilimi na musamman. *A kan samun lokutan Gwajin Ilimi na Musamman a Karon Farko ga Kowa da Kowa da na Ɗaiɗaiku (FIIE)* a nan (Kafa: https://bit.ly/3V5feWG).

# JAGORA GA IYAYE ZUWA GA SAMUN GURBI, BITA, DA MATAKAN KORA

## Kula Da Kananan Yara a Matakin Farko

Akwai damar samar da taimako ga iyalai masu jarirai da yara ƙanƙana da ba su girma da sauri. Hukumar da ke samar da aiyukan kulawa daga tushe a Texas ita ce Ma'aikatar Lafiya da Aiyukan Al'umma ta Texas. Shirin da aka tsara don yara ƙanana na Kula da Yara tun a Matakin Farko (**ECI**). Waɗannan ayyukan domin yara ne 'yan ƙasa da shekara uku.

A shekara uku, yaran da ke da lalura na iya samun damar yin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa. Idan haka ne, gundunmawar makarantar yaro ce ke da alhakin tabbatar da an samarwa yaro da FAPE a bukin cikar yaron shekara uku. Ba dukkan yara kan samu ayyukan ICI da cancanta da samun ayyukan da makarantar gwamnati ta samar ba. Haka zalika, aƙalla kwanakin kalanda 90 kafin ƙaramin yaro ya samu ayyukan ECI ya cika shekara uku, za a saka lokacin taron don taimakawa iyali miƙawa daga ayyukan ECI zuwa tsarin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, idan haka ya dace. Idan yaro ya cancanta, dole ne ilimi na musamman da ayyukan masu alaƙa su zama akwai su don yaro a ranar bukin cikar sa ko cikar ta shekara uku. *Beyond ECI* wallafa ce da ta ƙunshi bayani game da musaya daga shirin lokacin ƙurciya na farko zuwa tsarin ilmi na musamman. Wannan wallafar, *Bayan ECI* ana iya samun ta a nan [(Kafa: bit.ly/35G7y3E).](bit.ly/35G7y3E)

Yara daga haihuwa zuwa shekaru 3 suka cika sharaɗin cancanta bisa zamowa kurma ko masu ji sama-sama ko zamowa yaro mai gani garara-garara sun cancanci shirin ECI da ayyukan ilimi na musamman daga makarantun gwamnati. Ayyukan ilimi na musamman a makarantun gwamnati zasu rufa baya kuma su yi daidai da tanaje-tanajen ayyukan ECI ga waɗannan yaran.

## Ayyuka ga Yara Yan Shekaru Uku Zuwa Biyar (kafin shiga ƙaramar makarantar boko)

Kuma ƙofar taimako a buɗe take ga yara da suka cancanta da ke tsakanin shekara uku zuwa biyar, kuma ana kiran waɗannan ayyukan ilimi na musamman ga ƙananan yara (ECSE) Wasu daga cikin waɗancan yaran na fara samun hidimomi tun suna yan shekaru 3 a lokacin da suke daina samun hidimomin ECI kamar dai yanda aka yi bayani a sama. Saidai kuma, sauran an gwadasu da tantancesu bisa ga bayanan waɗanda suka kawosu kamar idan iyaye suka buƙaci haka idan suna da fargabar salon koyon karatu da girman yaronsu. Ana bada ayyuka na ECSE a wurare daban-daban, kuma a cikin ƙayyadaddun yanayi, wasu yara suna da damar yin rajista sau biyu a makarantu masu zaman kansu da tsarin makarantun gwamnati lokacin da suke da shekaru uku da huɗu.

## Taimako kan Shekarun koyon Yaro

Idan kana da damuwa game da halin koyo na ɗanka lokacin da yake shekarun makaranta (aƙalla shekaru 5 ko shekarun shiga makarantar rainon yara, ya kasance idan ƙasa da shekara 5), to mataki na farko shi ne ka yi magana da malamin ɗanka ko shugaban makaranta game da damuwarka. Idan ba a yi nasara a wannan matakin ba, ya kamata ka tambayi ma'aikacin makarantar game da yin magana zuwa ga ƙungiyar tallafin ɗalibai ta makarantar, wadda ƙungiya ce ta malamai da sauran ma'aikata da kan gamu su magance kowace matsalar ta shafi halayya ko koyo da yara kan fuskanta.

Tun farko, za a maida hankali wajen kulawa da bada aiyukan tallafi ga ɗaliban da ke fama da ajin neman ilmin bai-

ɗaya waɗanda aka kawo domin gwajin ilmi na musamman a ƙarƙashin Hukumar IDEA a maimakon karɓar kulawa da aiyukan tallafi. Idan ɗalibi ya ci gaba da fama da ajin neman ilmi na bai-ɗaya alhali ga tanajin kulawa da tallafawa, ko kuma ba za a iya biyan buƙatun ɗaliibi ta waɗannan kulawa da tallafawa ba, ko kuma duk lokacin da makaranta ta yi zargin ko ta ke da dalilin ta zargi samuwar nakasu da yuwuwar buƙatar ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi, dole ne makarantar ta tura ɗalibin don samun cikakken gwaji na mutum da mutum na matakin farko a ƙarƙashin IDEA. Ba a buƙatar a samarwa ɗalibi da taimako na wani ɗan lokaci gabanin a tura shi a matsayin cikakken mutum da tantancewar da aka yi da farko. Tura magana ko buƙata matsayin cikakken da tantancewar da aka yi da farko da watakila ma'aikacin makaranta kan yi a kowane lokaci, ko mai kula da doka, ko wani mutum da ke cikin sha'anin ilmi ko lura da ɗalibi.

## Shirin Tallafawa Mai Falle da Yawa, da ya shafi Amsa bukatar Neman Tallafi

Dole ne kowace makaranta ta samar da shirin tallafawa mai falle da yawa da ya shafi kulawa da aiyukan tallafawa da suka haɗa da tallafawa ta ɓangaren ilimi da wanin sa kamar gyaran tarbiyya. Amsa bukatar Neman Tallafi (**RtI**) dabara ce da makarantu da dama ke amfani da ita a shirinsu na MTSS Abubuwan asali na tsarin RtI su ne: tanadin kimiyya, umurnin a bisa bincike da shiga tsakani a bangaren ajin neman ilmi; sanya ido da ɗaukar matakai a kan ci gaban yaro masu dangantaka da shiga tsakani; da amfani da waɗannan matakan ci gaban don yanke hukunci a kan ilmi.

Dabarar Rti, wadda ɓangare ce na MTSS, shi ne inda duk mataki or falle ke nuna ƙarin tsanantar irin matakin agaji. Za a ci gaba da sauya tsarin shiga tsakanin da aka samarwa yaro a bisa matakin ci gaba da lura har sai yaron ya samu cikakken ci gaba. Yaran da ba su nuna alamun ci gaba a shiga tsakani na farko cikin wani iyakantaccen lokaci, kamar yadda bincike ya nuna, ana kiran waɗannan don shiga tsakani mai tsanani. Galibi, makarantarka na da wadatattun bayanai bayan mako shida na shiga tsakanin don yanke hukunci a kan matakai na gaba (m.s. ci gaba da shiga tsakani, tsananta shiga tsakani, sake dubawa). Lokacin da aka ɗauka don yanke hukunci ya dogara a yawa/tsawon lokacin shiga tsakanin da ƙwarewar da ake son cimma.

Yaro ba ya buƙatar ci gaba ta hanyar kowane matakin tsarin RtI kafin a miƙa shi don samun ilmi na musamman. Da zaran ta bayyana cewa shiga tsakani a kan ilmin bai-ɗaya bai wadata ba, to ya kamata ma'aikacin makaranta ya zargi cewa yaro na da lalura sannan dole ne a ɗauki matakin farko. Muhimman matakai wajen tantancewa idan har shiga tsakani akan ilimin bai-ɗaya sun wadata sun haɗa da sake duba tarihin shiga tsakanin da duba bayanan ci gaban ɗalibin (adadin ci gaba na yanzu da yunkurin cike gurbi). Iyaye kuma na iya neman izini a kowane lokaci koda kuwa yaro na samun kulawa ta hanyar tsarin RtI. Ba lallai a yi amfani da matakan RtI don jinkirta ko hana tantancewar lokaci akan yaron da ake zargi da lalura a tsarin IDEA ba. Karin bayani game da tsarin RtI (Kafa: bit.ly/3nDMTDu).

## Turawa tantancewa matakin farko

Haƙki ne da ya rataya a wuyan Makaranta da ta nemi yardarka da kuma gudanar da gwajin farko na ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa a duk lokacin da ta ke zargin cewa yaronka yana da nakasa kuma yana buƙatar ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa a ƙarƙashin IDEA. Kana iya neman tantancewar farko na yaronka a kowane lokaci.

Idan ka tura buƙatu a rubuce ga daraktan ayyukan ilimi na musamman na Karamar Hukumar Ilimi (**LEA's**) ko ga ma'aikacin gudanarwa na gunduma, kamar shugaban tsangaya, don gwajin farko don cancantar ilimi na musamman, to makarantar dole ne, ba a wuce ranar kwanaki 15 na karatu ba daga ranar da makarantar ta karɓi buƙatar, ko dai ta ba ka: 1) rubutacciyar sanarwa game da shawararta na bada izinin yin gwajin sai kwafin *Sanarwar*

*Matakan Kariya* (Kafa: fw.escapps.net), kwafin *Bayanin Ilimi na Musamman ga Iyaye* wanda Hukumar ta TEA ta ƙirƙira, da damar ba da izini a rubuce don kimantawa; ko 2) gabanin rubutaccen sanarwa na kin tantance ɗanka, kwafin *Sanarwar Matakan Kariya* (Kafa: fw.escapps.net), da wani kwafi na Bitar TEA ta samar da fom ɗin Ilimi na Musamman domin Iyaye Lokacin da makaranta ta soma shirin tura yaro dan gwaji, to wajibi ne kuma ta sanar da kai hakan.

Sai a lura cewa ana iya buƙatar samun ilmi na musamman ta hanyar maganar baki sannan babu buƙatar sai an rubuta. Dole ne makarantun gunduma da na masu zaman kan su ya zama sun yi daidai da sanarwar tarayya da buƙatar tantance, gano, da tantance yaran da ake zargi da lalura da ke buƙatar ilmi na musamman. Babu wani takamaiman lokaci da ake buƙata don mayar da martani ga buƙatar da aka yi da maganar baki, amma an ƙarfafa wa makarantu su bi tsarin lokaci na kwana 15 na makaranta kamar yadda aka bayyana a sama.

## Gabanin Rubutacciyar Sanarwa

Ɗaya daga cikin haƙƙoƙinka ƙarƙashin IDEA shi ne samun sanarwa a rubuce tun da farko game da wasu matakai ko kasawa da ya shafi tartibin lokacin yaronka kafin makaranta ta ɗauki mataki ko ta ƙi ɗaukar kowane mataki. Musamman, dole ne makaranta ta ba ka sanarwa a rubuce a cikin harshenka ko wata hanyar isar da saƙo ta daban yayin da ta:

- Shawartar soma ko canza alamar ganewa, tantancewa, shirin ilmi, ko samarwa yaronka gurbi ko tanadar FAPE ga yaronka (ciki kuwa har da sauyi da aka jawo ta soke izininka don ci gaba da samar da sahihin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa); ko
- Kin soma ko canza alamar ganewa, tantancewa, shirin ilmi, ko samawa yaronka gurbi ko tanadar FAPE ga yaronka.

Da farko ya zama dole a bayar da rubutacciyar sanarwa aƙalla kwana biyar na makaranta kafin fara aikin da makarantar ta bayar da shawara ko ta ƙi bayarwa har sai ka amince da gajeren lokaci da aka saka. Dole makaranta ta tanadar maka da sanarwa a rubuce kafin haka ko da kuwa ka amince da ko ka buƙaci canji.

Dole ne rubutacciyar sanarwar ta ƙunshi waɗannan bayanai:

(1) Bayanin aikin da makaranta ta bayar da shawarar dalla-dalla ko ta ƙi;
(2) Bayanin dalilin da ya sama makaranta ta bayar da shawarar ko ta ƙi ɗaukar mataki;
(3) Bayani dalla-dalla na kowace hanyar kimantawa, tantancewa, adana, ko rahoton da makaranta ta yi amfani da shi a matsayin hujjar shawarar ko ƙin ɗ ɗaukar mataki;
(4) Sanarwar cewa iyayen yaron da ke da lalura na da kariya a ƙarƙashin tsarin hanyar kiyayewa a wannan bangare, idan wannan sanarwa ba ita ce matakin da aka bayyana da farko ba, wannan na nufin ta yadda za a iya samun kwafin bayanin tsare-tsaren hanyar kiyayewa;
(5) Sassan da za a tuntuba na iyaye don a samu taimako a fahimtar abubuwan da ake buƙata na ilmi na musamman;
(6) Bayani dalla-dalla na wasu zabi da kwamitin ARD ya yi la'akari da su da dalilan da ya sa aka yi watsi da waɗannan zabin; da
(7) Bayani dalla-dalla na wasu abubuwa da ke da alaƙa da shawarar makarantar ko watsi da ita.

## Amincewar Iyaye

Akwai wasu ayyuka a cikin tsarin sha'anin ilmi na musamman da ba za su auku ba har sai makarantar ta samu

amincewarka. Dole ne makarantar ta sanar da kai dukan bayanan da ake buƙata domin yanke shawara mai kyau, da suka ƙunshi bayani dalla-dalla na aikin tsara shawarar.

Dole ne bayanan su kasance cikin harshenka ko wata hanyar isar da saƙo, sai fa idan akwai cikas isar da saƙon ta wannan hanya. Idan akwai bayanin da aka ajiye da ake son fitarwa, haka na nufin ka fahimta sannan ka amince a rubuce makaranta ta gudanar da aikin da ake neman amincewarka.

Yayin da ka amince, hakan na nufin cewa ka fahimta ka yarda a rubuce cewa makaranta ta gudanar da ayyukan da ake neman amincewarka. Yana da kyau ka fahimci cewa amincewar ta ganin dama ce kuma ana iya janyewa a kowane lokaci kafin aikin ya soma. Har ila yau, idan ka janye amincewar a kan wani aiki, ba za a sake dawo da ita ba.

Wadannan da ke tafe misalai ne na ayyukan da ake neman amincewarka:

- Tantance yaronka a karon farko;
- Sake tantance yaronka sau guda a shekara uku, ko yawan maimaita tantancewa idan har ana buƙatar bayanan, sannan ya zama kai ko malamin yaronka ne ya buƙaci sake tantancewar;
- Samar da ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa a karon farko;
- Yi ma mamban kwamitin ARD uzurin halartar taron kwamitin lokacin da taron ya ƙunshi sauyi ga ko tattauna sashen manhajar mamban ko ayyuka masu alaƙa; da
- Gayyatar wakili daga kowace hukuma don ya halarta wanda ke da alhaki samar da kuɗi ko biyan kuɗi ga ayyukan sakandire.

## Tsare-tsaren Tantancewa

Idan ka amince da cikakken gwaji na mutum da mutum (FIIE), wajibe ne makarantar ta fara samar ta matashiya a rubuce kan dukkan matakan gwajin da za ta gudanar. Dole ne makaranta ta yi amfani da dabaru da hanyoyin tantancewa daban-daban don tattara bayanai masu amfani da alaƙa, na ci gaba, sannan na ilmi game da yaronka, ciki har da bayanan da ka samar. Mai yuwa makarantar yaronka ba za ta yi amfani da kowane irin mataki ko kwatantawa ba a matsayin ma'aunin fahimtar ko yaronka na da wata lalura sannan da tunanin tsarin ilmin da ya dace da yaronka. Dole ne makarantarka ta gudanar da tantance yaronka a dukan sassa masu dangantaka da zargin lalura da ake don fahimtar idan yaronka na da lalura sannan da fahimtar buƙatarsa ko buƙatarta a kan ilmi. Dole tsarin tantance yaronka ya:

- Kunshi bayanai game da karatun yaronka, ci gaba, da ƙwazo;
- Ya zama an gudanar da shi ƙarƙashin kulawa da horon jami'i mai ilmi a bisa ƙa'idojin mai samar da gwajin, sannan ya zama an kula a bisa sahihan dalilan da aka tsara don tantancewa kuma da ake dogaro da su;
- Ya zama an gudanar da ita a cikin harshen yarona ko wata hanyar isar da saƙo sai fa idan ba mai yuwa ba ne; da
- Ya zama na rashin son rai ko an bayar da shi ta hanyar da babu cin zarafin yaronka; kome al'adarsa ko al'adarta, jinsi, ko lalura.

Horarrun ma'aikata masu ilmi da za su yi gwaji kan bambanta bisa la'akari da irin nakasar da ake zargi. Idan ana zargin cewa yaro na da matsalar karatu, da rubutu da haɗa baƙaƙe ko wata cuta makamanciyar wannan, to sai a sanya wani mahiri a ɓangaren cututtuka masu nasaba matakan karatu a cikin gwajin. Bugu da ƙari, dole ne kimantawar ta haɗa da wuraren da ake buƙata a cikin Littafin Jagora na Dyslexia na Hukumar Ilimi ta Jihar Texas. ([Kafa: https://bit.ly/3Z5uXrt](https://bit.ly/3Z5uXrt)) da Kundin Mulki na 19 na Jihar Texas(TAC) §74.28 ([Kafa: https://bit.ly/3YQcWMe](https://bit.ly/3YQcWMe)).

Dole ne a kammala tantancewar farko da sakamakon rahoton a cikin aƙalla kwana 45 na makaranta daga ranar da

makarantar ta samu amincewarka a rubuce. Sai dai kuma, idan yaronka ya kasance ba ya zuwa makaranta sau uku ko fiye da kwanakin makaranta a lokacin gwajin, za a tsawaita lokacin gwajin da adadin kwanakin makaranta daidai da adadin kwanakin makaranta da yaronka ba ya nan. Dole ne makarantar ta ba ka kwafin rahoton gwajin ba tare da biyan ko sisi ba, kuma da zarar an kammala shi amma bai wuce kwanaki biyar na makaranta ba kafin taron farko na kwamitin ARD na ɗanku don tantance cancanta.

Idan yaronka bai cika shekara biyar ba zuwa Satumba 1 na shekarar makaranta kuma ba a shigar da shi a makarantar gwamnati ba ko kuma ya yi rajista a makaranta mai zaman kanta ko makarantar cikin gida ba tare da la'akari da shekaru ba, ƙimar farko da rahoton da aka samu dole ne a kammala ba a baya fiye da ranar makaranta ta 45 ta biyo bayan ranar da makarantar ta sami izini a rubuce.

Sai dai ban da jadawalin ranar makaranta ta 45. Idan har makaranta ta samu amincewarka a rubuce a matakin tantancewar farko a cikin aƙalla kwana 35 amma ƙasa da kwanakin makaranta 45 kafin ranar koyarwa ta shekarar karatu, to ko dole ne a kammala rubuta rahoton sakamakon a kuma ba ka shi daga 30 ga Yuni na shekarar. Har ila yau, idan yaronka ba halarci makaranta ba a kwana uku ko fiye a lokacin tantancewar, babu buƙatar saka 30 ga watan Yuni. A maimakon haka, za a yi la'akari da jaddawalin gabaɗaya na kwanakin karatu 45 haɗi da ƙarin kwanaki uku ko fiye na rashin halarta. Idan makarantar ta sami izininka ƙasa da kwanakin 35 na makaranta kafin ranar koyarwa ta ƙarshe ta shekara, za a yi aiki da jadawali 45 na kwanakin makaranta 45, tare da tsawaita kwanaki uku ko fiye fashin zuwa aji a lokacin gwaji.

Idan ba ka amince da tantancewar farko ba, makaranta na iya, amma ba a buƙatar, bin diiddigin tantancewar ta hanyar neman shiga tsakani ko roƙon yin saurare. Idan makaranta ta yanke shawarar ƙin bin diddigin tantancewar, to fa makarantar ba ta karya ƙa'ida ba a ƙarƙashin tsarin IDEA don gane, bin sawu, da tantance dukan yara masu fama da lalura da ke buƙatar ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa. An tura wannan buƙatar zuwa ga makarantar *neman aikin yara*.

## Tarukan Kwamitin Shiga, da Bita, da Kora (ARD)

A cikin kwanaki talatin daga ranar da aka kammala rahoton gwajin farko, dole ne a kafa kwamitin ARD don yin la'akari da rahoton da kuma tantance ko yaronka ya cancanci neman ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi. Membobin kwamitin ARD su ne kamar haka:

- Kai, mahaifin;
- Aƙalla game-garin malami ɗaya na yaron wanda dole ne, idan zai yiwu, ya zama malami wanda ke da alhakin aiwatar da wani yanki na IEP na yaro;
- Aƙalla malamin ilmi na musamman ko wanda ya kawo yaron;
- Wakilin makarantar;
- Wani da zai fassara ayyukan da aka yi na sakamakon tantancewar;
- Wasu mutane da ke da ilmi ko wata ƙwarewa da ta shafi yaron kuma ko dai kai ko makaranta za ta gayyace su;
- Duk loakcin da ya dace, yaron;
- Gwargwadon ya dace, tare da amincewarka a rubuce ko, bayan yaronka ya kai shekara 18, tare da amincewar yaronka babba a rubuce, wani wakilin kowace hukuma da ta shiga aikin da ke da alhakin samar da ko biyan kuɗin ayyukan;
- Wani wakili daga sashen ilmin koyon aiki da fasaha, idan son samu ne malami, idan ana ci gaba da kula da yaron a matakin farko ko ci gaba da sanyawa a tsarin ilmin koyon aiki ko fasaha; da
- Kwararren ma'aikaci wanda ke cikin kwamitin tantance ƙwarewar harshe, idan an gano yaron a matsayin mai yare biyu a fagen koyo.

Haka kuma kwamitin ARD ya ƙunshi, kamar yadda ya dace:

- Wani malamin da ya ƙware a sashin ilmin ɗalibai kurame ko masu lalurar ji, idan har ana zargin yaron da kasancewa ko an rubuta shi a matsayin kurma ko mai fama da lalurar ji;
- Malamin da ke da takadar shaida a koyar da ɗaliban da ke da nakasar gani, idan ana zargin yaro yana da matsalar gani ko kuma wanda aka tabbatar a rubuce;
- Malamin da ke da takadar shaida a koyar da ɗaliban da ke da nakasar gani, idan ana zargin yaro yana da matsalar gani ko kuma wanda aka tabbatar a rubuce;
- Kwararren wanda ya cika buƙatun TEC, §29.0031(b), da 19 TAC §74.28, gami da Littafin Hannu game da Cutar Rashin Fahimta, idan ana zargin ɗalibin na da cutar Cutar Rashin Fahimta ko an gano hakan.

Dole ne makarantar ta gayyace ka zuwa kowane taron kwamitin ARD don yaronka ta kuma yi himmar ganin ɗaya ko duka iyayen yaron biyu sun halarta. Dole ne a bayar da sanarwar taron a rubuce aƙalla kwanaki biyar na karatu kafin taron sai fa idan ka amince da gajeren lokacin da aka saka. Dole ne rubutacciyar sanarwar ta ƙunshi manufa, lokaci, wurin taro, da jerin sunayen waɗanda zasu halarci taron. Idan ba ka iya magana da harshen Ingilshi, dole ne makaranta ta samar maka da sanarwar cikin harshenka sai fa idan hakan ba mai yuwa ba ne. Idan harshenka bai da tsarin rubutu, dole ne makaranta ta dauki matakan tabbatar da cewa an fassara sanarwar ta hanyar maganar baki ko ta wata hanyar da za ka iya fahimtar sanarwar.

Dole ne lokaci da wurin taron kwamitin ARD ya yi muku daidai kai da makaranta. Idan lokaci ko ranar da makaranta ta saka ba yi maka daidai ba, dole ne makaranta ta yi ƙoƙarin samar da wani lokaci da za ka iya samun damar halarta. Idan kowane daga iyaye ba ya iya halartar taron, kana iya halarta ta hanyoyin zabi kamar ta wayar tarho ko taro ta kafar bidiyo. Idan makaranta ta kasa gamsar da kai ka halarta, to sannan makarantar na iya gudanar da taron ba tare da kai ba.

Ana iya yi ma wani memban kwamitin ARD uzurin rashin halarta bangare ko dukan taron kwamitin ARD idan mutumin ba lalla sai ya halarta ba saboda sashin tsarin manhajar karantu ko ba a sauya ko tattauna wani aiki mai alaƙa a taron ba. Dole ka bayar da uzurin a rubuce.

Kuma memban kwamitin ARD na iya neman izini daga halartar taron kwamitin ARD lokacin da taron ya ƙunshi wani sauyi zuwa ga, ko tattaunawar, sashin tsarin manhajar karatu na memban ko aiki mai alaƙa idan kai da makarantar kun amince da uzurin a rubuce sannan mutumin da aka yi ma uzurin ya miƙa saƙon a rubuce a cikin tsarin ci gaba na IEP kafin taron.

## Cancanta

Akwai sassa biyu na gwaji da ke duba fahimtar ko yaronka ya cancanci samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa:
(1) dole ne yaronka ya zama yana da lalura da cancanta a ƙrƙashin IDEA; sannan (2) sakamakon lalurar, dole ne yaronka ya zama yana da buƙata da ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da zai more daga ilmin. Don cancanta ga bangare na farko na gwajin mai sassa biyu, yaron mai shekara tsakanin 3 zuwa 21, in ban da kamar yadda aka bayyana a ƙasa, dole ne ya cancanci samun nau'in lalura ɗaya ko fiye da aka lissafa:

- Galhanga;
- Kurma ko mai lalurar ji (shekaru daga haihuwa zuwa 21);
- Kurma-makanta (shekaru daga haihuwa zuwa 21);
- Damuwa mai kawo nakasa
- Tabuwar ƙwaƙwalwa;
- Lalurori na musamman;

- Kula da yarintar ɗaiɗaikun yara (shekara uku zuwa biyar)*;
- Jinkirin girma (shekara 3 zuwa 9)**;
- Matsalar ƙashi;
- Wasu lalurorin lafiya;
- Takamaiman lalurar gane abu;
- Lalurar magana ko koyon harshe;
- Rauni a ƙwaƙwalwa; ko
- Lalurar gani (shekara daga haihuwa zuwa 21).

*Ba za a yi amfani da Kula da yarintar ɗaiɗaikun yara ba daga shekarar karatu ta 2025-2026.
**Za a fara amfani da cancanta a ƙarƙashin jinkirin girma daga shekarar karatu ta 2024-2025.

Dole ne kwamitin ARD ya yi kyakkyawan ƙuduri cikin kwanakin kalanda 30 daga ranar da aka kammala rahoton tantancewar farko. Idan rana ta 30 ta faɗa a lokacin bazara kuma ba a aiki amakaranta, kwamitin ARD yana da har zuwa ranar karatu ta 15 a cikin bazara don kammala yanke shawara game da matakin cancantar farko, IEP, da sanyawa, sai dai idan gwajin farko ya nuna cewa yaron zai buƙaci ƙarin ayyuka na shekara ta makaranta (**ESY**) a lokacin bazara. Idan an nuna ayyukan ESY, dole ne kwamitin ARD ya taro gaugawa bayan kammala rahoton gwajin.

Ba dukan masu koyo da ke fama ne suka cancanci samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa ba. Idan babban abinda yaronka ya ke fama da shi ne rashin koyarwar da ta dace a karatu ko lissafi ko kuma saboda gaskiyar cewa ɗanka yana da cikas a ƙwarewar Ingilishi, yaronka ba dole ba ne a ƙaddara cewa ya zama yaro mai nakasa a ƙarƙashin IDEA. Idan tantancewar ta nuna cewa yaronka ba shi da lalura, tawagar goyon bayan na iya zama su bayar da shawarar yin wasu ayyuka daban ko shiraruwa ga dukan sassan ilmi don taimakon yaronka

Idan tantancewar ta nuna cewa yaronka na da lalura, to dole ne kwamitin ARD ya magance matsalar sashe na biyu na gwajin mai sassa biyu ta hanyar duba ko yaronka na buƙatar ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa don saka shi sannan a samar da ci gaba a manhajar dukan sassan ilmi (wato manhaja ɗaya ta yaran da ba su da lalura).

### Tanadin Ayyukkan Farko

Idan yaronka ya cancanci samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, za a buƙaci makaranta ta samarwa yaronka da tsarin FAPE a wuri mai yanayi maras kwaramaniya. A kan cimma wannan nasara ne ta hanyar ayyukan kwamitin ARD na IEP da tsarin ilmin makarantar na IEP. Kafin makarantar ta iya samar da kowane ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, har wa yau, dole ne ta samu amincewarka a kan ayyukan. Dole ne makarantar ta yi ƙoƙarin samun amincewarka don samar da ayyukan a matakin farko. Idan ba ka amince da tanadin ayyukan da farko ba, mai yuwa makarantar ba za ta nemi shiga tsakani ko buƙaci bin wata ƙa'idar sauraren dalilinka na ƙin amincewa da ayyukan ba. Babu wani ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da za samar muddin ka ƙi amincewa. Makarantar ba ta karya dokokin aikinta wajen samarwa yaronka da FAPE idan ka ƙi amincewa ko kasa mayar da martani ga buƙatar samar da amincewar a tanadin farko na tsarin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa.

## Assasa Shirin Gatanci na Neman Ilmi (IEP)

Manyan sassan IEP sun ƙunshi:

- Matakin nasarar karatun yaronka a yanzu da ƙwazonsa a aikace (**PLAAFP**);
- Kiyastaccen muradin shekara da suka haɗa da nasarar karatu da muradin ƙwazon aiki;
- Bayani dalla-dalla na tsarin ilmi na musamman, ayyuka masu alaƙa, ƙarin taimako da za a samar;

- Bayani game da yadda yaronku zai shiga cikin gwaji na jiha da na gundumomi, gami da bayanin kowane masaukin da ya dace wanda ya zama dole don yaronka ya yi jarabawa, da kuma ko yaronku yana buƙatar yin wata jarabawa ta dabam, maimakon tantancewar da aka saba yi a duk faɗin Jiha, da kuma dalilin da ya sa zaɓin madadin ya dace da yaronka;
- Ayyukan miƙawa, lokacin da ya dace da shekaru; da
- Dole ne a yi la'akari da wasu bangarori, sanna idan wajibi ne a ƙudurta, magance matsalar da yara masu lalura ke fuskanta, buƙatu, ko dalilai.

TEA ya samar da samfurin IEP (Kafa: bit.ly/3smMLMe). Makarantar yaronka na iya amfani da wannan samfurin ko na iya amfani da wani samfurin.

A cikin bunƙasa IEP, akwai abubuwa da dama da dole ne kwamitin ARD ya yi la'akari da su, da suka ƙunshi:

- Karfin yaronka;
- Kulawarka don ƙarfafa ilmin yaronka;
- Sakamakon sabuwar tantancewa game da yaronka; da
- Ilmi, na cigaba, da buƙatun aiki na yaronka.

Haka zalika, dole ne kwamitin ARD ya magance abubuwa na musamman ga wasu, kamar haka:

- Yin la'akari da amfani da tabbataccen shiga tsakani da taimako sannan wasu matakan magance matsalar wannan ɗabi'a lokacin da ɗabi'ar yaro ta hana yaro koyo ko ta wasu;
- Yi la'akari da bukatun yaren yaron kamar yadda waɗannan buƙatun suka shafi IEP na yaron lokacin da ya cancanci zama mai yare biyu na karatu; samar da koyarwa ta makafi da amfani da abin rubutun makafi, sai dai idan kwamitin ya yanke shawarar cewa koyarwar makafi ko amfani da kayan rubutun makafi bai dace da yaron ba lokacin da yaron ya kasance makaho ko yake gani garara-garara;
- Yi la'akari da bukatun sadarwa na kowane yaro da ke da nakasa, kuma ga yaron da kurma ne ko mai ji sama-sama, yi la'akari da harshen yaron da buƙatun sa na sadarwa, da damammakin sadarwa ta kai tsaye tare da takwarorinsa da ƙwararrun ma'aikata a cikin harshen yaron da yanayin sadarwa, matakin ilimi, da cikakkun bukatu, ciki har da dama don koyarwa kai tsaye a cikin harshen yaron da yanayin sadarwa;
- Yin la'akari da shin kowane yaro mai lalurar da ke buƙatar taimako na'urori da ayyuka; da
- Magance duk abubuwan da ake bukata a cikin Littafin Jagoran Cutar Dyslexia, idan an zartar, ga ɗalibin da aka gano da cutar dyslexia kuma wanda ke buƙatar koyarwar ta masu cutar.

## Na yanzu Matakin Nasarar Ilmi Ayukkan Himma

Dole ne IEP ya ƙumnhi bayanin PLAAFP na yaronka. Wannan bayanin dole ne ya ƙunshi yadda lalurar ta shafi shiga da kuma ci gaban dukan manhajar. Idan yaronka bai shiga makaranta ba, dole ne bayanin ya bayyana ta ya lalurar ta shafi shiga a cikin ayyukan da suka dace da shekaru.

## Muradun Shekara

Dole ne IEP ya ƙunshi ma'aunan burukan shekara, ciki har da burukan ilmi da aiki, da aka tsara su yi daidai da buƙatun yaro sakamakon lalura saboda haka za a iya saka shi ko ita a cikin tsarin ci gaba a dukan manhajar. Kuma dole ne a burukan su magance wasu buƙatocin na ilmi da kan taso sakamakon lalurar yaronka. Dole ne IEP ya bayyana dalla-dalla yadda yaronka ke samun ci gaba don auna cimma burukan shekara da lokacin da za a samar maka da rahotanni kan ci gaban.

## Ilmi Na Musamman, Ayyuka Masu Alaka, da Karin Taimako da Ayyuka

Kwamitin ARD kan yanke shawarar irin ayyukan da ake buƙata don:

- Ba yaro damar ci gaba yadda ya dace don cimma burukan shekara;
- Shiga sannan kawo ci gaba a tsarin manhajar ciki har da shiga ayyukan makaranta da ayyukan da ba na makaranta ba; da
- Ilmantu sannan kasance da yara marasa lalura.

Dole ne IEP ya ƙunshi bayani na buƙatar ilmi na musamman, ayyuka masu alaƙa, da samar da ƙarin taimako sannan da ayyuka ga yaronka ko a madadin yaronka. Dole waɗannan ayyuka su zama bisa nazarin bincike a kan takwarori ya zuwa gwargwadon iyawa.

Haka kuma, dole ne IEP ya ƙunshi bayanin kowane shiriin da ake buƙatar sauyawa da taimakon da jami'in makaranta zai samar. Dole ne IEP ya kuma ƙunshi ranar da aka saka don soma ayyukan da sauyin da lokacin da ake tsammani, wuri, da tsawon lokacin ayyukan da sauye-sauyen.

## Bayyana Kimantawa

A ƙarƙashin dokar tarayya, dole ne a ba dukan yara tsarin tantancewar jaha don iya gane ko makaranta ta yi nasarar koyar da yara nagartaccen ilmin jaha. A Texas, an san nagartaccen ilmi a matsayin Wadataccen Tsarin Ilmi na Texas da Dabaru, wanda a kan iya samu a shafin yanar gizo na TEA [(Kafa: bit.ly/3bFeuSk)](bit.ly/3bFeuSk). Yara da ke fama da lalura da suka samu ilmi na musamman za su samu tantancewar da ta dace ta jaha, ko dai wadda aka saba da ita ko wadda aka zaɓa don yara masu babbar matsalar fahimta da ta yi daidai da zaɓin tsarin ci gaban nagartaccen ilmi. Ba tare da la'akari da ko yaronka ya shiga tantancewar da aka saba da ita ko wadda aka zaba ba, tantancewar ta yi daidai da tsarin nagartaccen ilmin jaha mai cike da ƙalubale, sannan dole ne yaronka ya samu gurbin da ya dace a yayin tantancewa ta jaha da dukan gunduma, idan zai yuwu, kamar yadda aka nuna a IEP na yaronka.

Idan kwamitin ARD ya ga cewa masauki na da mahimmanci don yaronka ya shiga cikin gwajin, to dole ne IEP ta ƙunshi bayanin masaukin da suka dace. Bayanan masauki daga shafin yanar gizo na TEA [(Kafa: bit.ly/3sq2vht)](bit.ly/3sq2vht).

Idan kwamitin ARD ya yanke shawarar cewa dole ne yaronka ya yi wani gwaji na daban maimakon gwaji na musamman na jiha ko na gundumomi, to dole ne IEP ta haɗa da sanarwa game da dalilin da yasa yaron ba zai iya shiga cikin gwaji na yau da kullum ba, dalilin da yasa madadin tantancewar da aka zaɓa ya dace da yaron. Gudan fam ɗin sa hannu na tantancewar da TEA ta ƙirƙiro za a haɗa shi a matsayin wani ɓangare na IEP ɗin ɗanku a wannan yanayin. Haka kuma, idan har yaronka ya shiga tantancewar da aka saba da ita, to dole ne IEP na yaronka ya ƙushi ko maƙasudi manufofin ɗan lokaci. Ana buƙatar maƙasudi ko manufofin dan lokaci kawai ga yaran da ke fama da matsananciyar lalurar koyo da ke shiga tsarin tantancewar zabi da ya yi daidai da tsarin zabi ci gaban nagartaccen ilmi.

## Miƙawa

IDEA da dokar jaha ta nemi cewa IEPs ga manyan ɗalibai kan magance canjin ayyukan. *Sauyin* tsarin ayyuka ne da aka haɗe da tsarawa don taimakawa yaro ci gaba daga makaranta zuwa ayyukan bayan makaranta. Shekarun da wannan tsarin canji kan soma, har wa yau, sun bambanta a ƙarƙashin tsarin doka na tarayya da jaha. Don haka, dokokin kwamishina a ƙarƙashin 19 TAC §89.1055 suna buƙatar ayyukan miƙa mulki na tarayya da na jiha don farawa kafin taron farko na IEP.

Zai fara aiki lokacin da ɗalibi ya cika shekara 14 da haihuwa. Don haka, bai wuce taron IEP na farko da zai fara aiki lokacin da ɗalibi ya kai shekaru 14, dole ne kwamitin ARD yayi la'akari kuma ya magance batutuwa masu zuwa a cikin IEP idan hakan ya dace:

(1) Shigar ɗalibi mai dacewa a cikin tsarin canjin ɗaliban zuwa gudanar da rayuwa a wajen tsarin marantar gwamnati;
(2) Sa hannu irin wanda ya dace na iyaye da wasu jama'ar da aka gayyata a harkar tura ɗalibin.:
    a. Iyayen ɗalibi; ko
    b. Gundumar makarantar da aka saka ɗalibi;
(3) Zaɓuɓɓukan karatun da suka dace na gaba da sakandare, gami da shirye-shiryen aikin kwasa-kwasan matakin gaba da sakandare;
(4) Tantance tsarin aikin sana'a da ya dace;
(5) Yanayin da suka dace don gudanar da tsarin tura dalibi ko iyayen ɗdalibi zuwa ga hukumar gwamnati don ayyuka ko amafanin jama'a, ciki har da turawa zuwa ga hukumar gwamnati don maye gurbin ɗalibin a jerin sunaye da ake jiran fitar sa ga jama'a da ɗalabai; da
(6) Amfani da samun dacewa:
    a. Karin taimako, ayyuka, zagaye, da wasu damarmaki da kan taimaki ɗalibi ƙirƙirar dabarub ci gaba; da
    b. Taimako da ayyuka don ɗaukaka 'yancin ɗalibi da ƙudurin kai, ciki har da yarjejeniyar yanke hukunci da ta samu goyon baya.

A soma tun kafin taron farko na IEP ya fara aiki lokacin da ɗalibin ya cika shekaru 14, ko ƙasa da haka idan kwamitin ARD ya ƙaddara ya dace, IEP dole ne ya haɗa da:

1. Ka tsara ƙididdigaggen ma'aunin maƙasudin da za a cimmawa a makarantar gaba da sakandare bisa la'akari da shekarun da suka dace da gwaji da suka shafi horo, ilimi, aiki, kuma, inda ya dace, ƙwarewar rayuwa mai zaman kanta; kuma
2. da ayyukan tura ɗalibii, da suka haɗa da darussan karatu, da ake buƙata don taimaka wa ɗalibin don cimma burin gaba da sakandare.

A soma tun kafin taron farko na IEP ya fara aiki lokacin da ɗalibin ya cika shekaru 18, dole ne kwamitin ARD ya yi la'akari, kuma idan har ya dace, ya dace, ya magance matsalolin IEP da suka haɗa da:

1. Sa hannun iyayen yaro da wasu jama'ar a tura yaro da kuma harkokinsa na nan gaba, idan iyayen ko wasu jama'ar:
    a. Ɗalibi ya gayyace su su hallarra ko gundumar makarantar da aka saka ɗalibi; ko
    b. Ko da amincewar ɗalibin ya hallara a ƙarƙashin yarjejeniyar da aka amince da ita; and
2. Samar da mahallin koyarwa da suka dace da shekaru, gami da yanayin al'umma ko muhallin da ke shirya ɗalibin don karatun gaba da sakandare ko horo, aikin da ake ruguguwar samu, ko rayuwa yanci, wanda haka ya yi daidai da manufofin tura ɗalibin da manufofinsa.

Ya kamata yaronka ya halarci taron kwamitin ARD lokacin da za a tattauna burin ayyukan tura shi gaba da sakandare. Ida yaronka bai halartar taron, to dole ne kwamitin ARD ya ɗauki matakai don tabbatar da an yi la'akari da abubuwan da yaronka ya fi mayarwa hankali da sha'awa. Sa hannu irin wanda ya dace na iyaye da wasu jama'ar da aka gayyata a harkar tura ɗalibin.: Bugu da ƙari, gwargwadon ya dace, tare da amincewarka a rubuce ko, bayan yaronka babba a rubuce, dole ne makaranta ta gayyaci wani wakilin kowace hukuma da ta shiga aikin da ke da alhakin samar da ko biyan kuɗin ayyukan.

## Manyan Ɗalibai

Lokacin da yaronka ya kai shekara 18, yaron ya zama *babban ɗalibi*. Ɗalibai manya na da damar yanke hukunci da kanu face sai idan doka ta lura hakan ba daidai ba ne. A ARD kwamiti kan yi taro shekara guda aƙalla kafin yaronka ya kai shekara 18, yaronka zai fahimci cewa damar yanke hukunci za ta sauya daga iyayensu zuwa gare su. Dole ne IEP na yaronka ya ƙunshi bayani don gano cewa iyaye da kuma yaran na da masaniyar sauya haƙƙin. Kuma dole ya ƙunshi bayanin da zai bayyana dalla-dalla abubuwan da aka bayar game da lura, zabin lura, da bayanan da aka raba game da taimako da ayyuka da aka tsara su taimakawa zaman cin gashin kai.

Lokacin da aka sauya haƙƙin zuwa ga babban ɗalibinka, kai da babban ɗalibinka za ku samu sanarwarda ake buƙata nan gaba. Haka kuma, sanarwar kwamitin na ARD ba gayyata ba ne gare ka na ka don halarci taruka. Kana halartar taruka ne kawai idan har babban ɗalibinka ne ya gayyace ka ko ya ba makaranta izinin gayyatar ka.

## Yara Masu Galhanga

Ga yaron da ke da In'ina, akwai dabaru 11 waɗanda, ḏaidai da ƙuduri na 19 na TAC §89.1055(g), dole ne a yi la'akari da su aƙalla kowace shekara, dangane da nazarin ɗan adam, ayyukan shirin karatu na tushen bincike gwargwadon iya aiki. Idan akwai buƙata, dole ne a tattauna waɗannan dabaru a cikin tsari IEP. Yayin da ba buƙata kuma, to dole ne IEP ya ƙunshi bayanai a rubuce a kan haka da dalilin da ya sa aka yanke hukuncin. Haka ƙarin dubarun da kwamitin ARD ya wajaba ya yi la'akari su ne:

- Kara tsawon lokacin shirin ilmi;
- Tsare-tsaren lokaci na kullum da zai shafi mafi ƙanƙantar loacin da ba a tsara ba and active engagement in learning activities;
- Horon cikin gida da na al'umma, ko ta wani zabi daban;
- Dabarun goyon bayan ɗabi'a;
- Shirin lokacin gaba;
- Horon iyaye/iyali, da goyon baya;
- Rabon daidai na ma'aikaci-da-yaro da ya dace da ayyukan da aka gano;
- Shiga tsakanin sadarwa;
- Taimako a kan Dabarun zamantakewa da dabaru;
- Kwararre a ilmi/ tallafin ma'aikaci; da
- Dubarun koyarwa a bisa nazari na tsara, ayyukan bincike.

## Yara Kurame ko Masu Lalurar Ji

Ga yaro kurma ko mai lalurar ji, dole ne kwamitin ARD ya yi la'akari da na yaron:

- Harshe da buƙatun isar da saƙo;
- Damarmakin isar da saƙo kai tsaye tare da tsara da wani ƙwararre a fannin harshen yaro da tsarin isar da saƙo;
- Matakin ilimi; da
- Yaron da ke da tarin buƙatu, da suka ƙunshi damarmakin umurnin aiki na kai tsaye a fannin harshen yaro da tsarin isar da saƙo.

## Yara Makafi ko Masu Lalurar Gani

A ƙarƙashin dokar jiha, ga yaron da ya ke makaho ne ko mai lalurar gani, dole ne kwamitin ARD ya saka ƙa'idojin

aikin na IEP na yaro a cikin karatun makafi sannan a yi amfani da abin karatun makafi sai fa idan kwamitin ARD ya ƙuduri kuma ya bayyana cewa abin karatun makafin bai hanyar koyon karatu da ta dace da yara ba ce. Fahimtar da kwamitin ARD ya yi dole ne ta zama bisa tantancewar dacewar hanyar lkoyar da yaro karatu da dabarun koyo na buƙatun yaro na yanzu da na gaba.

A ƙarƙashin dokar jaha, da ta bayyana yaron da ya ke makaho ko mai lalurar gani, dole ne kwamitn ARD ya yi la'akari da buƙatar yaro:

- Basirar diyya, kamar abin karatu na makafi da tsara ra'ayi, da wasu dubarun da ake buƙata don samun damar kai ga sauran manhajoji;
- Gabatarwa da ƙa'idojin tafiya;
- Basirar zamantakewar da juna;
- Tsarin aiki;
- Fasahar taimako da ta ƙunshi na'urorin gani;
- Dubarun dogaro da kai;
- Wasanni da abubuwan jin daɗi;
- Azamar kai; da
- Karfin azanci.

## Tsarin Gyaran Tarbiyya da Kulawa (BIP)

Idan kwamitin ARD ya fahimci cewa shirin shiga tsakanin akan halaye ko BIA ya dace da yaronka, cewa dole ne a haɗa da wannan shiri a matsayin wani sashi na IEP na yaronka sannan an samar da shi ga kowane malami mai alhakin koyar da yaronka

## Karin Lokacin Ayyukan Makaranta (ESY)

Dole kwamitin ARD ya yi la'akari da idan yaronka ya cancanci samun ayyukan ESY a bitar shekara-shekara na IEP ɗin yaronka. Dole ne a rubuta buƙatun ayyukan ESY na amfani da bayanan da kai da gundumar ku ka tattara ta yin amfani da gwaji na a hukumance da na gida. Yaronka ya cancanci ayyukan ESY idan, a ɗaya ko ma fiye daga cikin mahimman wurare da aka magance a cikin manufofin IEP na yanzu na ɗanka inda yaron ya nuna cigaba a baya, yaronka ya baje kolin, ko kuma ana iya sa ran nunawa, mai tsanani ko babban koma baya wanda ba za a iya dawowa cikin lokaci da bai tsawaita ba. Kalmar *mai tsanani ko koma baya* yana nufin cewa yaron ya kasance, ko kuma ba zai iya ci gaba da samun ci gaban da aka samu a baya ba a ɗaya ko fiye da mahimmancin yankunan IEP idan babu ayyukan ESY.

Idan kwamitin ARD ya ƙaddara cewa yaronka yana buƙatar ayyuka na ESY, to dole ne IEP ta gano wuraren da za a magance yayin ayyukan ESY. Ana buƙatar kwamitin ARD don tattauna buƙatar ayyukan ESY a taron nazarin IEP na shekara-shekara na yaro.

## Cike Gurbi

IDEA na buƙatar cewa yaron da ke da lalura a ilmantar da shi a cikin *muhalli maras matsi da yawa*. Wannan na nufin cewa dole a ilmantar da yaranka da ba su da lalura gwagwardon yadda ya dace. Cire ɗanka daga yanayin karatu na gabaɗaya na iya faruwa ne kawai idan yanayi ko tsananin nakasarsa ta kasance ba za a iya samun karatu a cikin azuzuwan na yam gaba ɗaya tare da amfani da ƙarin kayan taimako da ayyuka masu gamsarwa ba.

*Karin kayan taimako da ayyuka* na nufin taimako, da ayyuka, da sauran tallafi waɗanda ake bayarwa a cikin azuzuwan ilimi na gabaɗaya, sauran yanayi da suka shafi ilimi, kuma a cikin tsarin ilimi da na ilimi, don ba da damar yara masu nakasa su sami ilimi tare da yara marasa nakasa cif-cif yanda ya dace.

Muhimmin sashi na sha'anin ilmi na musamman ya ƙunshi fahimtar gurbin ilmin da ya dace don inganta IEP na yaro. *Bada aji* na nufin yawan maki tare da ci gaba da zaɓin aji (watau azuzuwan ilimi na gabaɗaya, azuzuwan na musamman, makarantu na musamman, koyarwar gida, koyarwa a asibitoci da cibiyoyi) da ke akwai ga yaro mai nakasa. Samar da gurbi ba ya nufin wuri na zahiri na musamman ko wurin da za a yi ayyukan. Kwamitin ARD kan lura samar da gurbin ilmi a bisa IEP na yaron.

## Matakin Kwamitin ARD

Matakin kwamitin ARD game da abubuwan da ake buƙata na IEP dole ne ya zama membobin kwamtin sun amince da shi idan zai yuwu. Ana kiran wannan yarjejeniya sasantawa. Ya kamata kwamitin ARD ya aiki don cimma sasantawar, amma makaranta ke da cikakken alhakin tabbatar da cewa IEP ya ƙunshi ayyukan da yaronka ke buƙata don ya samu FAPE. Ba a yarda ba a yanke hukunci kan kwamitin ARD ta hanyra jefa ƙuri'a. Dole ne IEP ya nuna ko kai da mai jagoranta sun yarda ko ƙin amincewa da sahawarar kwamitin ARD.

Idan har ba ka yarda da shawarar kwamitin ARD ba, to za a ba ka dama ɗaya tak don sake lokacin da kwamitin ya saka baya kada ya zarce kwana 10 na karatu sai fa idan kai da makarantar kun cimma wata matsaya ta daban. Idan ka amshi tayin sake lokacin don sake taron, to dole ne kwamitin ARD ya saka lokacin sake taro a cikin lokacin da kowa ya amince da shi. Har ila yau, idan yaronka yana nan a sansani mai alamar hatsari ga yaronka ko wasu, ko idan yaronka ya aikata laifin kora ko laifin da ka iya kai ga maye gurbi a cikin tsarin kwamitin ladabtarwa, to kwamitin ARD ba zai sake lokaci ba ko da kuwa ba ka amince da matakin kwamitin ARD ba.

A yayin sake lokacin, dole ne memba ya yi la'akari da zabi, tara ƙarin bayanai, shirya samar da ƙarin takardu, da/ko samun ƙarin wasu mutane da za su iya taimakawa kwamitin ARD cimma manufa ɗaya.. Idan kwamitin ARD ya sake zaman taro sannan ka ci gaba da ƙin amincewa, sai ƙin yardar ya ƙun shi tanadin da aka yi da farko na ayyukan da ake buƙatar amincea kan su, dole ne makaranta ta zartas da IEP cewa makarantar ta yanke shawarar da ta dace ga yaronka.

Idan ba a cimma matsaya ba, dole ne a haɗa da rubutaccen bayani a cikin IEP kan dalilin ƙin amincewar. Idan ka ƙi amincewa da shawarar kwamitin ARD, to dole ne a ba ka damar rubuta naka bayani na ƙin amincewar. Dole ne tun da farko makaranta ta samar maka da sanarwa a rubuce aƙalla kwana biyar na karatu kafin zartas da IEP sai fa idan ka amince a cikin gajeren lokaci.

Kwamitin ARD na kuma iya zabar sauya dalilai a maimakon kasa cimma matsaya game da dukan abubuwan IEP da ake buƙata.

## Kwafin IEP

Dole ne makaranta ta ba ka kwafin rahoton tantance yaronka kuma a kyauta. Karƙashin Kundi na 19 na TAC §89.1055(r), idan ba za ka iya yin Turanci ba kuma yarenau na asalin Sipaniya ne, dole ne makarantar ta bada rubutaccen kwafi ko rikodin na sauti na IEP ɗin ɗanka da aka fassara zuwa Sipaniyanci. Idan ba za ka iya magana da Ingilishi ba kuma yarenka na asali ba Sipaniyanci ba ne, dole ne makarantar ta yi ƙoƙari sosai don samar da rubutaccen kwafi ko rikodin na sauti na IEP ɗin ɗanka da aka fassara zuwa yarenka na asali. Idan ba ka iya magana

da Ingilishi kuma harshenka bai da tsarin rubutu, to dole ne makaranta ta ɗauki matakai don tabbatar da cewa an fassara IEP na yaronka ta hanyar baki ko ta wata hanya a cikin harshenka. Fassara a rubuce na nufin cewa duka rubutu an fassara shi a ciki IEP na yaronka. Makaranta na iya samar maka da murya da aka naɗa na taron kwamitin ARD idan mai fassara ya taimaka maka ko fassarar zaman taron, da zarar an fassara IEP na yaronka a baki ko tsarin naɗin sauti.

Dole ne makarantar ta ɗauki duk matakan da suka dace don tabbatar da cewa iyaye sun fahimci abin da ake yi a taron kwamitin ARD, gami da shirya mai fassara ga iyayen da kurame ne ko ba su ji sosai ko kuma waɗanda Ingilishi ba shi ne harshensu na asali ba.

## Sake Duban IEP

Dole ne kwamitin ARD ya zauna aƙalla sau guda a shekara don sake duba IEP na yaronka sannan da lura da ko an cimma burukan shekara. Kwamitin ARD na iya gudanar da taro akai-akai fiye da shekara-shekara don yin bitar IEP na yaronka, kamar yadda ya dace, don magance:

- Kowace irin kasa cimma ci gaba ga burukan shekara da kuma gabaɗayan mahajar karatu;
- Sakamakon ko wace sake tantancewa;
- Bayanai game da yaro da aka samar ga, ko ta, iyayen;
- Buƙatar da yaron ke son cimma; ko
- Wasu lamurra.

Kana iya neman kwamitin ARD ya gudanar da taro don tattauna lamuran da suka shafi ilmin yaronka. Dole ne makaranta ta amshi buƙartarka a rubuce don gudanar da taron ko, kuma cikin kwana biiyar na makaranta, ta samar maka da sanarwa a rubuce tare da bayyana dalilin da ya sa makaranta ta ƙi kiran taro. Idan ba ka iya magana da harshen Ingilshi, dole ne makaranta ta samar maka da sanarwar cikin harshenka sai fa idan hakan ba mai yuwa ba ne. Idan harshenka bai da tsarin rubutu, dole ne makaranta ta dauki matakan tabbatar da cewa an fassara sanarwar ta hanyar maganar baki ko ta wata hanyar da za ka iya fahimtar sanarwar.

Kai da makaranta na iya amincewa da yin sauye-sauye ga IEP ba tare da gudanar da taron kwamitin ARD ba. Har ila yau, dole ne ya zama an gudanar da sauye-sauyen ga ƙudurin cancanta, sauye-sauyen samar da gurbi, da na bayyana manufa duk a taron kwamitin ARD. Idan IEP ya sauya a wajen taron kwamitin ARD, to dole ne a samar da takarda a rubuce da ta nuna amincewa akan sauyin. A bisa buƙata, dole ne makaranta ta samar maka da kwafi na sake bitar IEP tare da gyaran da aka saka ciki. Kari ga haka, dole ne makaranta ta tabbatar da cewa an sanar da kwamitin ARD na yaronka game da sauye-sauyen.

## Tantancewa

Da zarar yaronka ya soma samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, to akan buƙaci sake tantancewa lokaci zuwa lokaci. Dole ne makarantar ta yi ƙoƙarin samun amincewarka don sake tantancewa. Idan ka kasa mayar da amsa duk ƙoƙarin da aka yi, to makaranta na iya gudanar da sake tantancewar ba tare da amincewarka ba. Idan ka ƙi mayar da amsa don sake gudanar da tantance yaronka, makaranta na iya, ba a buƙatar yin, tambayar neman shiga tsakani ko buƙatar saurаren da ya dace don soke rashin amincewarka ka halarrci sake tantancewar. Makaranta ba ta karya dokar hakkin yaro ba ko wajibcin da ke kanta na tantance yaronka idan har makarantar ba ta nemi a soke ƙin amincewarka na halartar tantancewar ba.

Sake tantancewa iri ɗaya ce da tantancewar farko. Dole ne sake tantancewar ta zama ingantacciya don gano ko

yaro na ci gaba da nuna lalura da sauran buƙatar tallafin ilmin yaronka. Sai fa idan kai da makaranta kun yarda da akasin haka, to dole ne sake tantance yaronka ya kasance an yi ta akalla duk shekara uku. Ba a samun sake tantancewa fiye da su guda a cikin shekara sai fa idan kai da makaranta kun yarda da akasin haka.

Tantancewar bayanan gwaji da ke akwai (**REED**) dole ne a gudanar da shi a matsayin tantancewa matakin farko, idan har ya dace, dole ne tsarin tantance bayanan da ke akwai reed ya auku a matsayin sashin kowace irin tantancewar yaron da ke ƙarƙashin tsarin IDEA. Ba a buƙatar makaranta ta samu amincewarka wajen bitar bayanan tantancewar da ke akwai. Dole ne REED ya gudanar da taron kwamitin ARD, madamar wannan ne gwajin farko ko kuma kwamitin ARD idan za a sake gwaji, ciki har da kai, amma babu dole sai ya wakana a lokacin taron. Dole membobi su yi bitar bayanan da ke akwai game da yaronka, ciki har da bayanan da ka samar, da ka ƙudurta iyakacin tantancewar ko sake tantancewar.

Idan tun asali yaronka na samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, kwamitin ARD kan yanke shawarar wace ƙarin tantancewa, idan har akwai, akwai buƙatar ƙarin wasu ko yin sauye-sauye ga tsarin ilmin yaronka na musamman da ayuka masu alaƙa.

Idan har kwamitin ARDA ya yanke shawarar cewa babu buƙatar ƙarin tantancewa don gano ko yaro na ci gaba da buƙatar ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, dole ne kuma a bayyana dalilan wannan matakin. Bayan bayyana dalilan da ya sa kwamitin ARD ya yanke hukuncin cewa bayanan tantancewar da ke akwai yanzu sun wadatar, to makaranta ba ta buƙatar gudanar da sabuwar tantancewa don kammala tantancewar da ake buƙata sai fa idan ka buƙaci makaranta ta yi haka.

## Tantancewa Ilmi Mai Zaman Kanta (IEE)

Idan ba ka amince da makaranta ta tantance ko sake tatancewar ba, kana iya neman IEE a ciki kuɗin makaranta. Dole ne makaranta ta ba ka bayani game da in da za a samu IEE sannan dole ne ta ba ka kwafi mai ɗauke da sharuɗɗan makaranta don samun IEE. Dole ne IEE ya cika sharuɗɗan makaranta. Idan ka nemi IEE, dole ne makaranta, ba tare ɓata lokaci ba, ko dai a biya kuɗi don IEE ko neman sausare don nuna cewa tantancewarta da dace. Ka cancanci samun IEE ɗaya kawai a cikin kuɗin jama'a kowane lokaci makaranta ta gudanar da tantancewa. Idan makaranta ta buƙaci saurarenn sannan jami'in kula da saurarenn ya yanke shawarar cewa tantancewar da makaranta ta yi ya dace, har yanzu kana da haƙƙin samun IEE, amma ba makaranta za ta biya ba. Dole ne kwamitin ARD yayi la'akari da bayanan da aka samu daga IFF da suka yi daidai da sharuɗɗan makaranta su dace da tanadin FAPE ko da kuwa ba makaranta ba ta biya IEE ba.

## Janye Ayyukan Don Amicewa

Kawai dai kamar yadda kake da ikon amincewa da tanadin farko na ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, kana da ikon janye amincewarka ga ayyukan. Dole ne janyewarka ga amincewar ta zama a rubuce. Da zarar makaranta ta samu janyewarka a rubuce, dole ne ta girmama matakinka. Har ila yau, kafin makaranta ta dakatar da ci gaba d a ayyukan, dole ne ta samar maka da sanarwa a rubuce cewa za a tsayar da ayyukan. Duk da ya ke dole ne makaranta ta dakatar da ayyukan, makaranta ba bukatar yin gyara ga bayanan da aka adana na yaronka don cire kowane damar yaronka a baya na samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa a lokacin da ya gabata.

Idan ka soke amincewar ka na cigaba da samar da ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi, to yaronka ba zai cancanci kowane ɗayan kariyar da ke ƙarƙashin IDEA ba. Bugu da ƙari, idan ka janye amincewarka don ayyukan, mai yuwa makaranta ba za ta nemi shiga tsakanin ko saurare ba da zimma sauya ko ƙalubalantar matakin ba.

## Kammalawa

Ɗaya daga cikin manufofin tsarin ilmin jama'a a Texas shi ne duk ɗalibai za su kasance a makaranta har sai sun samu babbar takardar shaidar difloma. Dole ne ɗalibai su samu wata daraja domin su kammala da samun babbar difloma. Ga yaron da ya samu ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, dole ne makaranta ta bi wasu hanyoyi a yayin shirin yaye ɗalibi ko kawo ƙarshen ba ɗalibin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa saboda ɗalibin bi cika sharuɗɗan shekaru ba da ake buƙata ba. Bugu da ƙari, kwamitin ARD na taka muhimmiiyar rawa a matakai masu alaƙa da kammala karatru.

Karƙashin IDEA, ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi, dole ne su kasance suna samuwa ga yaro ko babban ɗalibin da ya cancanta har zuwa ya kammala karatunsa ko ya wuce shekarun cancantar da ake bukata don karatu a makarantun gwamnati da suka dace a ƙarƙashin dokar jiha, wanda waɗannan su ne masu shekaru 21 a Texas ko har zuwa ranar haihuwar ɗalibin ta cika 22. Babban ɗalibin da ke karɓar ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi wanda ya cika shekaru 21 a ranar 1 ga Satumba na shekarar karatu, ya cancanci a yi masa hidima a ƙarshen wannan shekarar karatu ko har sai ya kammala karatunsa tare da difloma ta babbar makaranta bisa cika ka'idodin manhaja da yawan makin da ya dace ga ɗalibai a cikin karatun gabaɗaya, ala ayyi halin, duk wanda dai ya zo na farko.

Lokacin da cancantar samun ilimi na musamman ke ƙarewa ga ɗanka ko ta wani babban ɗalibi sakamakon kammala karatunsa da takardar shaidar kammala sakandare ko kuma saboda wuce shekarun cancantar ilimi na musamman da ayyukan da ke da alaƙa da shi, dole ne makarantar ta ba ka sanarwa a rubuce na ƙarewar ayyukan. Bugu da ƙari, dole ne makarantar ta ba yaron ko ɗalibi babba taƙaitaccen bayanin sakamakon karatunsa ko karatunta da ƙwazon da aka nuna, wanda zai haɗa da takardar yabo akan yadda za a taimaki yaron ko babban ɗalibin cimma burukansa na gaba da sakandire.

Wanda ya sami ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi, imma yaro ko babba, kuma iya kammala karatunsa kuma a ba shi takardar shaidar difloma ta babbar makaranta ta hanyar biyan ma'auni iri ɗaya da buƙatun ƙirƙira da ya dace ga ɗalibai a cikin ilimin gabaɗaya, da kuma wuce abubuwan da ake buƙata na jihar (wanda zai iya haɗa da yanayin da ɗalibin ya yi ƙoƙari amma ya kasa samun gamsasshen matsayi a ƙasa da biyu daga cikin gwajin da ake buƙata na jihar).

Duk ɗaliban da suka kammala karatun digiri waɗanda suka cancanci ilimi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi waɗanda cancantarsu ta ƙare saboda samun takardar shaidar kammala sakandare, dole ne a ba su ƙwarya-ƙwaryar takardar bayanin nasarorin ilimi da aiwatar da aiki. Dole ne a yi la'akari da wannan taƙaitawa, kamar yadda ya dace, ra'ayin iyaye da ɗalibi da yabo a rubuce daga wasu hukumomin lura da manya akan yadda za a taimakawa ɗalibi cimma burukansa na bayan kammala sakandire. Ga wasu ɗalibai, dole ne taƙaitawar ta ƙunshi tantacewar ɗalibin.

Yaro ko babban ɗalibi wanda ya cika sharuɗɗan samun digiri daidai da 19 TAC 89.1070(b)(2) ko (b)(3)(A), (B), ko (C) kuma yana ƙasa da shekara 22 yana da haƙƙin samun ingantaccen ilimin jama'a kyauta ƙarƙashin IDEA. Yaron na iya, a ƙarƙashin wasu dalilai, samun komawa makaranta ya samu ayyuka har zuwa ƙarshen shekarar karatu da shi ko ita suka kai shekarar 22 da haihuwa. Idan yaronka yana neman komawa bayan ya cika sharuɗɗan samun digiri kuma an ba shi takardar shaidar difloma, dole ne kwamitin ARD ya fayyace ayyukan ilimi da ake buƙata.

## Ladabtarwa

Akwai ƙa'idoji na musamman da ke akwai don matakan ladabtarwa da a kan ɗaukarwa yaro mai fama da lalura. Gabaɗaya, ba za a iya cire yaro mai fama da lalura daga wurin karatunsa ko karatunta na yanzu fiye da kwana 10 a jere idan wannan rashin ɗa'ar na da alaƙa da lalur da yake ko take fama da ita. Bugu da ƙari, wasu matakan ladabtarwa da ke da nasaba da ɗalibi mai fama da lalura kan taso da buƙatar taron kwamitin ARD.

### Cirewar Gajeren Zango

Jami'an makaranta na iya cire yaronka daga gurbin karatu na yanzu idan yaronka ya karya dokar ɗabi'a ta ɗalibai. Wannan cirewar na iya zama wani wuri daidaitacce na zabin tsarin ilmi na wucin gadi (**IAES**), wani wuri, ko dakatarwa da ba ta wuce kwana 10 ba a jere gwargwadon matakin ladabtarwar da ya shafi yara da ba su fama da lalura, sannan da ƙarin cirewar da ba zarce kwana 10 a jere na karatu a wannan shekarar karatu, ga wasu abubuwan da suka faru na daban akan rashin ɗa'ar da zarar cirewar ba ta haddasa wani sauyin samar da gurbi ba. Galibi an bayyana wannan a matsayin *ƙa'idar kwana 10*.

Cirewar ladabtarwa ta tsawon kwanan karatu 10 a jere ko ƙasa da haka ba ya haddasa buƙatar gudanar da taron kwamitin ARD, sai idan cirewar ta haddasa wani sauyin samar da gurbi. Gundumar makaranta ba ta samar da ayyuka ga yaro mai fama da lalura ko yaron da bai fama da lalura da aka cire daga gurbinsa ko gurbinta na yanzu tsawon kwana 10 jere ko ƙasa da haka a wannan shekarar karatu.

### Jimlar Cirewa Zuwa Kwanaki 10 ko Fiye

Jami'an makaranta na iya yin odar ƙarin cirewa mai gajeren-zango a wannan shekarar karatu akan wasu abubuwan da suka faru na daban na rashin ɗa'a, muddin waɗannan cirewar ba za su haddasa wani sauyin samar da gurbi ba. Bayan an cire yaronka tsawon kwanakin karatu 10 a jere a wannan shekarar karatu, to idan cirewar da aka yi a yanzu ba ta zarce kwana 10 ba kwanakin karatu a jere sannan ba sauyin samar da gurbi ba ne, dole ne makaranta ta samar da ayyuka don ba yaronka damar ci gaba da hallara a cikin dukan tsarin manhajar karatu, koda yake a wani tsari, sannan don ya sa mu ci gaban cimma buruka da aka saka a IEP na yaron. Dole ne ma'aikacin makaranta ya tuntubi aƙalla ɗaya daga malaman yaronka don tantance waɗanne ayukka ake buƙata. A lura cewa IDEA na buƙatar a 34 CFR §300.530(d)(5) cewa kwamitin ARD na ƙudurta ayyukan da suka dace idan cirewar ta sauyin samar da gurbi ce.

### Sauyin Samar da Gurbi

Cire yaro mai fama da lalura daga gurbinsa ko gurbinta na karatu ya zamasauyin samar da gurbi idan cirewa ta zarce kwanan karatu 10 a jere ko yaron na da jerin cirewar da ta zama wata mai yawa. Zubin cirewar kan faru lokacin da:

- Adadin cirewar da ta zarce kwana 10 na ranakun karatu a shekarar karatu;
- Hallayar yaro ta fi kama da halayyar yaro a lokacin abubuwan da suka faru a baya da suka haddasa yawan jerin cirewar; sannan
- Wasu abubuwa kamar tsawon lokacin cirewar, adadin lokacin da aka cire yaro, da kusancin tsakanin wata cirewar da wata.

Makaranta na iya fahimtar abin a bisa dalilin rikici-kan-rikici ko dai cirewa barkatai ta haifar da sauyi na samar da gurbi. Kana iya ƙalubalantar matakin da makarantar game da ko cirewar barkatai ta faru ne ta hanyar sauraren lamarin da kuma tsarin shari'a.

Idan makaranta ta yi nufin cirewar da ta za haifar da sauyin samar da gurbi, to dole ne jami'an makaranta su sanar da kai matakin sannan su samar maka da kwafin Sanarwar Tsare-tsaren Kariya (Kafa: fw.escapps.net). Dole ne a yi wannan a ranar da aka ɗauki matakin sauyawa yaron gurbi. Bugu da kari, dole ne makaranta ta gudanar da taron kwamitin ARD don gudanar da abinda ake kira bayyananniyar ƙaddara. Dole nea yi taron ƙaddamar da bayyanarwa a cikin kwanakin karatu 10 daga ranar da aka yanke shawara don canza ajin yaron.

## Bayyanawar Kudurori

A lokacin gudanar da *bayyanawar ƙaduri*, dole ne kwamitin ARD ya yi bitar dukan bayanai masu alaƙa a fayil na yaronka, ciki har da IEP, kowane sanya idon malami, da kowane bayani mai alaƙa da ka samar don ƙudurta:

- Idan halin da ake tababa ya faru saboda, ko yana nuna alaƙa ta kai tsaye zuwa ga, lalurar da yaronka ke fama da ita; ko
- Idan halin da ake tababa kai tsaye ya faru ne saboda kasawar yaron ya nuna IEP ne.

Idan kwamitin ARD ya ƙudurta cewa an cimma kowane da waɗannan sharuɗɗa, to halin na da alaƙa lalular yaron. Idan har kwamitin ARD ya lura cewa babu wani sharaɗin da aka cimma, to halin ba ba shi da alaƙa da lalurar yaron.

## Lokacin da Hali ya Bayyana

Idan halin ya bayanna daga lalurar yaronka ne, to dole ne kwamitin ARD ya ko dai:

- Gudanar da aikin Kimanta Hali (**FBA**), sai fa idan makaranta ta gudanar da shi a baya kafin wani hali sakamakon sauyin gurbi ya faru, sannan ya aiwatar da BIP; ko
- Idan tun asali BIP na nan, yi bitar BIP sannan ka sauya shi yadda ya dace don magance matsalar halayyar.

Haka kuma, dole ne kwamitin ARD ya dawo da yaronka ga gurbin da aka cire shi sai fa idan:

- Kai da makaranta kun yarda da sauya gurbin a wani ɓangaren sauya BIP na yaronka; ko
- Karya dokar da yaronka ya yi na halayyar ɗalibai ya ƙunshi ɗaya daga cikin muhimman yanayin da aka bayyana a ƙasa.

Idan kwamitin ARD ya kai matsayar cewa kasawar makaranta ce sanadin ɗabi'ar yaronka don zartas da IEP, dole ne makaranta ta ɗauki matakan gaggawa don magance gazawar.

## Lokacin da Hali Bai Bayyana ba

Idan ɗabi'ar ba daga lalurar yaronka ba ce, wani jami'in makaranta na iya ladabtar da yaronka daidai da yadda aka yi wa sauran yara, sai fa idan ya zama wajibi za a ci gaba da aiwatar da wasu ayyukan ilmi. Kwamitin ARD na yaronka zai ƙudurta IAES da yaronka zai yi.

## Al'amurra Na Musamman

Jami'in makaranta na iya cire yaronka zuwa ga IAES har zuwa tsawon kwanakin karatu 45 ba tare da lura da ko halayyar daga lalurarsa ko lalurarta ne a inda yaronka ya ke:

- Ɗaukar ko mallakar makami a makaranta, cikin harabar makaranta, ko a lokacin karatu;
- Mallakar ko amfani da haramtattun ƙwayoyi da gangan ko sayar da ko shiga cinikin abubuwan da aka haramta a lokacin da ake makaranta, a harabar makaranta, ko a lokacin da ake karatu; ko
- Ya haddasa wa wani mummunan rauni a jiki a lokacin makaranta, a harabar makaranta, ko lokacin da ake karatu.

Kwamitin ARD zai ƙudurta IAES da yaronka zai yi.

### Kariya ga Yara da Har Yanzu Ba su Cancanci kai ga Samun Ilmi Na Musamman da Ayyuka Masu Alaka ba

Idan an lura yaronka bai cancanta samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa ba amma ya shiga wasu halaye da suka karya dokar hali kan ɗalibi, to yaronka na da haƙƙi samun tsarin kariya a cikin shirin IDEA idan makaranta ta san cewa yaronka na fama da lalura kafin faruwar lamarin. Ana samun ƙarin bayani game da wannan sha'anin a cikin Sanarwar Tsare-tsaren Kariya (Kafa: fw.escapps.net).

## Sauraren Bahasi Na Gaggawa

Idan ba ka amince da matakin ba dangane da gurbi a cikin IAES ko bayananniyar ƙaddara, kana iya neman a gudanar da zaman sauraren bahaasi na gaggawa. Kuma makarantar na iya neman sauraren bahasi idan tana son ƙalubalantar sake dawowar yaronka a makaranta bayan kwamitin ARD ya yanke hukuncin cewa halinsa ko halinta na da danganta da bayyananniyar lalurarsa ko lalurarta.

## Sulhunta Jayayya

Daga lokaci zuwa lokaci, ana iya samun jayayya dangane da tantancewa, gwaji, gurbin karatu, ko wani tanadin FAPE ga yaronka mai fama da lalura. Idan an samu rashin yarda, kana da ƙwarin guiwar yin aiki tare da jami'in makaranta don samar da daidaito. Kana iya tambayar makaranta game da wane irin tsarin sulhu shirin kan bai wa iyaye. Tsarin TEA kan samar da zabi hudu don samar da sulhu ga jayayya da ta shafi ilmi na musamman: tsarin IEP na sauƙaƙawa na jahar, ayyukan shiga tsakani, shirin samar da sulhu game da koke akan lamurran ilmi na musamman, da shirin sauraren bahaasi.

Ana iya samun bayanai game da jayayyar zaɓin sulhu a tsarin TEA a cikin *Sanarwar Tsare-tsaren Kariya* (Kafa: fw.escapps.net). Ana iya samu ƙarin bayani game da samar da sulhu akan jayayyar ilmi na musamman a shafin yanar gizo na TEA (Kafa: bit.ly/3bL6n73).

## Karin Taimako

Don samun cikakken jerin bayanan a taƙaice da aka samu a cikin wannan kundi, ziyarci shafin yaran gizo na Tsarin Shari'a (Kafa: bit.ly/3oIsKNS).

Akwai kwafi-kwafi na wannan takardar a sauran yaruka a shafin yanar gizo na SPEDTex (Kafa: bit.ly/3qorCzg).

Kuna kuma iya neman kwafi daga masahawarcin makaranta ko sashen ilmi na musamman na makaranta.